UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

# AMFANI DA REDIYO DON SADARWA DA AL'UMMOMI

**REDIYO WATA MUHIMMIYAR KAYAN AIKIN SADARWA CE A LOKACIN AIKIN AGAJI. GA WASU SHAWARWARI DON LA'AKARI DASU KAFIN AMFANI DA REDIYO DON SADARWA DA AL'UMMOMI DA ABUN YA SHAFA.**



## A INA ZA'A FARA?

- Aiwatar da binciken buƙatun bayanai da sadarwa don sanin yanayin amfani da rediyo. Rediyo na iya zama wani kayan aiki mai ƙarfi saboda yana ko'ina, yana da sauƙin amfani, da kuma yadda yake shawo kan cikas na ilimi.
- Ya daɗe da haryanzu tsofaffin mutane daga cikin al'umma na amfani dashi, amma kuma ba wai ya tsufa can da har matasa su bar shi ba (Rediyo ta intanet - ko rediyo na shafin yanar gizo - na tashi sosai).
- Bayan binciken, shirya wani dabara wanda yake la'akari da kowane ƙaluɓale da ake fuskanta. Shin akwai kowane rukunai jama'a da suke da matsalar samun damar rediyo? Shin akwai bambancin harsuna wanda zai sa a buƙaci yin shirye-shirye a harsuna daban-daban? Shin al'ummar gari na cikin wa'yanda ake nufa?
- Tantance yadda zaka aiwatar da dabarar ka. Galibi fara tashar rediyo na iya zama wani mataki mai bada tsoro idan baka saba da fasahar ba ko dokokin watsa labarai.
- Akwai littattafai hannu masu bayani sosai daban-daban akan batun (Kamar wannan sigar daga ICRC)



## SHIRYA FILIN

- Musaya da sauran ƙungiyoyi kuma musamman gwamnati da masu kula da dokokin sadarwa. Tabbatar hukumomin suna goyon bayan shirin.
- Misali, Rediyon First Response tawagar su nada kwarewa sosai a wannan fannin. Sun riga sun tattauna da masu kula da dokoki a ƙasashen da suke aiki saboda su iya ƙafa tashar rediyo bisa doka kuma su kaddamar dashi a cikin sa'o'i 72 na faruwar wani yanayin gaggawa. Abun burgewa, ko ba haka ba?

- Anan zaku samu jerin dukkan masu kula da dokokin sadarwa. Kowace mai kulawa da dokokin na bada bayanai akan shafin su game da ire-iren lasisin rediyo da kuɗaɗen su.

- Waɗannan kuɗaɗen na iya bambanta daga farashi mai sauƙi sosai zuwa farashi mai tsada ta amfani da tsarin lissafi mai wuya wato algorithm don lissafa farashin bisa ga jama'ar da akw nufa, karfin yaduwa, lambobin tashar, da sauransu.

## REDIYO BA TARE DA YADAWA

- Amma kuma, yi la'akari da amfani da sauti a matsayin wani kayan aiki na sadarwa, koda za'a wallafa bayanin akan FM ko ba za'ayi ba. Duba wannan takardar don ƙarin bayani akan ƙirƙiro bayani da murya.

- Za'a iya sake amfani da sakonnin murya, a wallafa kuma baya buƙatar na'urori da yawa (kowane kwamfuta da/ko babban waya). Za'a iya watsa waɗannan sakonnin a cikin gari ta lasifika ko akan abun hawa kamar babura.

- Yawancin rediyo na yanzu na haɗe da wuraren sanya USB ko memori, kuma hakan na nufin cewa za'a iya sauraran sauti da aka yi rikodi ba tare da kama FM. Yi tunanin rabs rediyo ga gungun masu sauraro na musamman, ko kuma al'umma gabadaya, bisa ga kuɗin da ake dashi, tasirin da ake nema, da farashi a kasuwa mai samuwa.

- Akwai kamfanonin da suke haɗa rediyo musamman don yanayin aikin agaji (kamar Freeplay Energy ko Lifeline Energy). Kuma akwai masu yin rediyo da dama masu farashi mai sauƙi wanda ake samu a kasuwanni na gida.

- Na'urori masu amfani da rana nada ƙarin faidodi: suna da tasiri kaɗan akan muhalli kuma yana taimakawa da rage farashi kamar siyan batura.

## KAYAN AIKIN REDIYO

### Kayan

#### *Kayan Aikin Rediyon FM*

Akwai na'urorin watsa labarai ta rediyo, eriya da kayan aiki a kasuwanni na ƙasa da ƙasa amma wasu kayan aiki an tsara su musamman don ƙungiyoyin agaji.

## FICHE PRATIQUE




- Ga wasu kamfanonin na ban sha'awa:
  - Pocket FM : na'ura watsa labarai ta rediyo wanda zai zauna daidai cikin jaƙa da ake rataya a baya, layi don samun intanet na 3G, zaɓin shigar da tauraron dan adam, Wifi da GPS. Karfin Watsawa: har zuwa 25W.
  - Rediyon First Response: Radio in a Suitcase - An riga an sanya duk manhajoji da ake buƙata a cikin kwamfutan tafi da gidanka. Karfin watsawa: har zuwa 600W.
  - AAREFF – AAREFF yana haɗa duk abubuwan da zaku iya buƙata, da la'akari da sauƙin riƙewa.

- Karfin na'urar watsa labarai ta rediyo shine ɗaya daga cikin abubuwa masu mahimmanci wajen tantance nisan yaɗuwa. Da fatan za'a lura: yayin ƙaruwar ƙarfin na'urar watsa labarai ta rediyo, dole fanel ɗin tare hasken rana shima yafi ƙarfi.

- Yi hattara da dokokin kwastam na ƙasar: Zai yiwu babu na'urorin watsa labarai na FM a kasuwanni na gida kuma akwai dokokin hana shiga/fitar da shi. Nema taimako daga abokanai aikin ka masu kawo kaya.

- Kuma zaka buƙaci gini mai tsayi ko hasumiya. A wasu wurare, wani ɗan tudu zai isa. Akwai jagororin yadda za'a ta yanar gizo wanda zai taimaka maka da wannan.

### *Kayan aikin shirya sauti*

- Ana samun waɗannan kayyayakin nan da nan a mafi yawan ƙasashe: na'urorin haɗa sauti na analog ko dijital, makirufo, na'urar jin sautin kunne, na'urorin ɗaukan sauti na tafi da gidanka, manyan wayoyi, kwamfutan tafi da gidanka, kayan aiki na hana ƙara, kujeru da suka dace da kuma hadda alamar "on air" mai fitila!
- Kar ku manta batun wayoyi daban-daban da kuma abun haɗa wayoyin: yawanci makarufo suna amfani da XLR, amma idan kana amfani da waya 3.5mm, zaka buƙaci abun haɗawa.

### *Makamashi*



- Idan kana wani wuri mai nesa inda babu tabbacin wutar lantarki, bambanta hanyoyin samun wuta kamar hasken rana tare da janareta a ajiye.

- Tabbatar baka wahalar da kayyayakin ka da rashin isasshen wuta. Wata kila za'a buƙaci karin kayan aiki yayin da tashar ke girma.

- Hadda fanel na hasken rana, inverter, batura, da na'urar kula dasu, kar ka manta ka hada da extension (yi hattara, amma, da rashin wuta) da kuma sanya kariya ga tsarin gabadaya ta binne wayoyin da ya kamata cikin ƙasa (tsawa nada haɗari sosai).

**FICHE PRATIQUE**



## Manhajoji

- Akwai manhajoji da yawa na kyauta da wanda ake biya don yin rikodi da tace bayani, sasu a jeri, cancanza tsakanin masu gabatar da shirye-shirye na radio da abubuwan da aka yi rikodi.
- Manhajar mai mahimmanci da zaka buƙata shine manhajar na watsa labarai. ZaraStudio wani manhajar ne mai sauƙi wanda yake da sigar na kyauta da wanda za'a biya mai ƙarin abubuwa.
- Audacity wata manhaja ce da ake amfani da ita wajen daukar sauti da kuma tacewa. Kayan aiki da ake biya kamar Adobe Audition na bari ku samu kwararren haɗi mai inganci
- Shin ko kun san cewa zai yiwu ku watsa labarai ta rediyo daga wayar ku? Akwai wasu manhajoji masu sauƙin amfani na Manyan wayoyi.



## Lasisi

- Farkon mataki shine binciken lasisi daban-daban da akw dashi: lasisin rediyo na ɗai-ɗaikun mutane wanda basu kware ba, lasisin ƙungiyoyin al'umma da NGOs, lasisin yan kasuwa...
- Wasu hukumomi ba bada lasisi na wucin gadi koda ƙungiyoyin basu da rajista na gida.
- Idan kana shakka, tuntubi lauyoyin ka. Kuma, kar ka ji tsoron aiki ta haɗin gwiwa; wasu ƙungiyoyi sun kware a wannan fannin kuma zasu iya taimaka maka.

**Ga wasu tambayoyi da za'ayi la'akari dasu:**

- Shin ana buƙatar duk kayyayakin suna ajiye kuma suna aiki kafin a yi aiki akai?
- Shin neman lasisin yana buƙatar ziyara zuwa fili daga hukumar?
- Menene ka'idodin biya?
- Shin ana buƙatar duba kayan aikin watsa labarai? Idan haka ne, daga wanene?
- Shin akwai kuɗi da za'a biya don nema?
- Yaya ake lissafa kuɗin lasisin?
- Menene tsawon lokacin lasisin?

UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

# MATAKI 5 DON FARAWA

## 1. YI AIKI TA HAƊIN GWIWA

- Haɗu da ƙungiyoyin da suke aiki a rediyo na gida, na yankin ko na ƙasar. Aiki da kafafun watsa labarai na gida don tabbatar da hanyar tattaunawa da al'ummomi, horar da yan gudun hijira akan jaridanci, shirye-shiryen rediyo ko wallafa bayanai
- Akwai ƙungiyoyin ƙasa da kasa - wanda yawancin su mambobin Cibiyoyin CDAC (kamar BBC Media Action, Internews, International Media Support, Fondation Hirondelle, MiCT...).

**SHAWARA:** Yi magana da wa'yanda za'a iya haɗin gwiwa dasu kuma yi tunanin yadda waɗannan haɗin gwiwa zai dace da shirin ka.

## 2. TATTARA KAYAN

- Fara ta amfani da sauti da dabaru daban-daban kafin koma kan watsa labarai ta rediyo.
- Yi amfani da dama duk damarmaki na gida da na ƙasa da ƙasa don neman kayan da kake buƙata. Wasu lokuta akwai yarjejeniya na doguwar lokaci tsakanin ƙungiyoyi don samun kaya da wuri

**SHAWARA:** Fara ta neman kwamfutan tafi da gidanka da kuma makirufo mai arha. Saukar da manhajar Audacity kuma fara rikodin da tace bayanai da ya dace da al'ummomi.

## 3. DUBA LASISIN

- Yin binciken abubuwan da ake buƙata don lasisin da kuma tasirin da wannan zai yi akan dabarar ka.

**SHAWARA:** Fara hira da hukumar sadarwa yau. Kana iya tantance wani irin lasisin kake buƙata, menene farashin, ka'idodin cancanta da hanyoyin nema.

## 5. MULKI

- Ya kamata a sa ido kan shirye-shirye don daidaitawa; ya kamata abubuwan da ake darajanta wajen sauya bayanai yazo daidai da na al'ummar.
- Yi tunani game da bayanan aiki ga matsayi daban-daban kuma sanya su tare cikin wani kwangilar "wanene zai yi menene".
- Kuma fayyace yadda za'a gudanar da kirayekiraye masu shigowa da gudunmawa (wato kai tsaye ko wanda an riga anyi rikodi).

**SHAWARA:** Akwai misalai da dama game da ƙafa da mulkin tashoshin rediyo. Zaku iya samu ƙarin bayani kan wannan batun anan.

## 6. SAURARO DA JAWO HANKALI

- Bayan ɗan lokaci, za'a iya haɗa ƙungiyoyin sauraro don tattauna abubuwan da suke faruwa a halin yanzu (gungun ɗai-ɗaikun mutane da suka haɗu don sauraro da tattauna abubuwan da aka watsa ta rediyo/sauti)

**SHAWARA:** Tuntubi al'umma da wuri don ganin wanene ya kamata a shigar dashi. Gano dabaru da kwararru game da kafafun watsa labarai da/ko jaridanci. Cigaba da mu'amala da waɗannan mutane kuma cigaba da tattauna dasu har shirin ta kare. Ta binciken ka, gano dabi'un al'umma na muamala da tashoshin rediyo.

Plus d'outils
et de conseils
pour communiquer avec les communautés sur le site : cwc.westafrica.exposed